


Zomo da Sauran Dabbobi
Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 4
Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.


Zomo da Sauran Dabbobi
Hausa Nigeria


Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/


http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su.
ISBN


Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright:  SIL International 2009






Zomo yana kiwo a ƙofar gida.
Sai ya hango kura a tafe.
Kura tana cin ƙananan dabbobi.
Zomo ba ya son kura ta cinye shi.







Zomo ya tsere da gudu.
Ya tafi gidan akuya.


Yana son akuya ta ba shi wurin ɓoyo.
Akuya tace ita ba ta da wurin ɓoyo.









Zomo ya tafi gidan jaki.
Yana son jaki ya ba shi wurin ɓoyo.
Jaki ya ce shi bai da wurin ɓoyo.







Zomo ya fito daga gidan jaki.
Ya tafi gidan doki.

Yana son doki ya ba shi wurin ɓoyo.
Doki ya ce shi bai da wurin ɓoyo.





Zomo ya fita daga gidan doki.
Ya tafi gidan kare.
Yana son kare ya ba shi wurin ɓoyo.
Kare yace shi bai da wurin ɓoyo.








Zomo ya fita daga gidan kare.
Ya tafi gidan tunkiya.
Yana son tunkiya ta ba shi wurin ɓoyo.
Tunkiya tace ita ba ta da wurin ɓoyo.

Zomo ya yi yawo ya gaji.
Bai samu wurin ɓoyo ba.
Sai ya yi tunanin ya ɓoye da kansa.
Don kar kura ta cinye shi.





Zomo ya ɓoye a cikin haki.
Kura ta shiga cikin gari.
Ta cinye sauran dabbobi duka.
Ba ta ga zomo ba.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK